# MUJALLAR CITAD RADIO
## RADIYON DA ZAKU SAURARA
www.citad.org/radio

Volume 1, issue 9

05-12-1442 AH
16-07-2021 AD


***CIBIYAR BUNKASA FASAHAR SADARWA DA CIGABAN AL'UMMA (CITAD) NA BAYAR DA HORO KAN ILIMIN NA'URA MAI KWAKWALWA***

# CITAD TA HALARCI TARON KUKA FELLOWSHIP

Cibiyar Kukah tare da hadin gwiwar Cibiyar




Bunkasa Fasahar Sadarwa da Cigaban Al'umma (CITAD), da Open Society Initiative of West Africa (OSIWA), Global Rights da Yar'adua Foundation sun gudanar da tattaunawa mai taken " Kafafen Yada Labarai da Kare hakkin yan kasa. '

An gudanar da tattaunawar a ranar 29 ga Satumba, 2021, a Cibiyar Taro ta Duniya dake Abuja.

An yi wannan tattaunawar ne don inganta hanyoyi da dabarun kare jama'a. da yadda za'ai aiki da ƙwararrun kafofin watsa labarai da ƙwararrun masu niyya don tattaunawa mai ma'ana game da dunƙule yanayin hakkin yan kasa.


Ta kuma yi karin haske kan yadda wannan murkushewar ke yin barazana ga dimokradiyyar Najeriya, tare da bayar da shawarwari kan dabarun ci gaba.

## LABARAN CIKI


| | |
|---|---|
| **Muryar Matasa** | 1 |
| **Watch Dog** | 2 |
| **Ilimin 'Ya Mace** | 3 |
| Sharhin Yau da Kullum | 4 |
| **Shiri Na Mussamman** | 5 |
| **Siyasa Da Rayuwa** | 6 |
| **Ilimi Da Matasa** | 7 |


**Zaku iya sauraro da sauke manhajar CITAD RADIO ta wannan likau din dake kasa**



*https://play.google.com/store/apps/details?id=com.citad.org&hl=en&gl=US*

# NIGERIA @61: ADAM ABDURRAHMAN YAKUB

A satin daya wuce ne, kasata Nigeria tayi bikin samun ‘yanci kanta daga hannun mulkin mallakar turawa, Shekara 61 data wuce.

Nigeria ta fara tafiya a matsayin kasa mai cikakkiyar ‘yanci wacce tafi ko wacce kasa yawa a yankin Africa,babban burin magabatan ta irin su Ahmadu Bello, Nnamdi Azikwe da kuma Obafemi Awolowo shine cigaban kasa ta ko wanne fanni.

Amman shekara 61 da aketa gwagwar maya, Nigeria ta rabune kan banbance-banbancen addini, kabilanci da kuma gurbataccen tatalin arzikin kasa.

Banbace-banbacen mu da ya tsolewa wasu ido ya zama shine ke farautar mu. Mafarkin mu na Zama kasa ‘daya mafi chigaba da kuma girma ya shafe. Burin matasanmu shine su samu karamar dama su tsallake kasashen waje, amma fa ni



***Adam Abdurrahman***
***Dalibin Digiri Na biyu a jami’ar***

na yarda da cewa Nigeria zata shawo kan lamarin kuma mafarkinmu na zamowa masu gaskiya. Ina mai bawa yan Nigeria hakuri musammam ma matasa da su hada kai dan samar da chi gaban kasar.

Nigeria tanada albarkatun kasa da na dan adam wadanda suke kirkire kikire kuma suke haskawa a idan duniya amma duk da haka mune babban birnin talauci na duniya da kuma yawan yaran da basa samun zuwa kamaranta.

Imaninmu bai rushe ba, ammafa sai suwagabannin kasar sun kirkira sabbin siyasa da dabaru da zasu gama da matsalonin tsaro, tattalin arziki da kuma walwalar yan kasa. Dole ne kuma gwamnati ta tashi tsaye wajen samarwa da matasa damar fafatawa da yan uwansu matasa na kashashen duniya tinda sune manyan gobe.

# SHIRIN ILIMIN ‘YA MACE

Shirin Ilimin Ya Mace wanda ke maida hanakli kan irin fadi tashi da mata ke samu musamman a bangaren da suka da ilimi, lafiya, kimiya da sauran bangarori na rayuwa.

Wannan satin shirin ya samu bakuncin Maryam Ibrahim Sani, Co-Chair Youth, National Coalition on Youth, Peace and Security Agenda in Nigeria. Wadda muka tattauna da ita akan Hanyoyin Inganta Ilimin Mata.

Gazzali Haruna Ibrahim ne ke gabatar da shirin a duk ranar talatar sati.



## Daga Al'ummar Mu: Gazzali Haruna Ibrahim

Shirin daga Alummarmu na wannan mako ya samu bakuncin Abdullahi Muhammad Nasiru dalibi daga jami'ar Bayero wanda yake karantar Na'ura maikwakwalwa, wanda muka tattauna dashi akan gudummawar da dalibai ke bayarwa a bangaren yaki da cinhanci da rashawa.

Shirin yana maida hankali ne kan yadda matasa pke hangen al'umma da kuma tunanin da suke da shi na ganin an samu mafuta kan abub uwan da suka shafi al'ummar .

Shirin na zuwa ne duk ranakun laraban mako.




# Martabar Ya Mace

Ku Kasance da Gidan Rediyon Express akan mita 90.3 a gobe Talata 5 ga watan Oktoba domin sauraron shirin Martabar Ya Mace da misalin ƙarfe 11:00am zuwa 12:00PM wanda ya ke wayar da kan al'umma akan illolin da ke tattare da cin zarafin mata da ƙananan yara.

A wannan makon shirin zai karɓi baƙuncin Samira Usman Adamu shugabar Society For Girl Child Care Ambassadors inda za ta yi bayani akan rawar da kowa zai iya takawa wajen yaƙi da cin zarafin mata da ƙananan yara a cikin al'umma.

Shirin Martabar Ya Mace shiri ne da cibiyar bunƙasa fasahar sadarwa da cigaban al'umma CITAD tare da tallafin gidauniyar Ford Foundation da ke ƙasar Amurka su ka ɗauki nauyin kawo muku.



WWW.CITAD.ORG/ RADIO

Main Office:3rd Floor, NSITF Building, No.1A, Social Insurance Road, Behind Trade Fair Complex, Zaria Road, Kano. P.O. Box 10210, Kano, Nigeria.
GSM: 080-68078282
080-54362931
070-33427467
E-mail: info@citad.org,
Website: www.citad.org

**www.citad.org**

**Center For Information Technology and Development**

**BABBAN EDITA**
Hamza Ibrahim

**EDITA**
Buhari Abba Rano

**MATAIMAKIN EDITA:**
Gazzzali Haruna

**MAI KULA DA TSARE-TSAREi:**
Ali Sabo

**Mai Kula Da Dab'i**
Salim Sani Shehu

***Domin Karin bayani a tunubi wannan imel din info@citad.org ko kuma lamabar waya 08026082162***

# TALLE

